JAGORA AKAN SHUGABANCI

***NA***

AYYUKAN KULA DA LAFIYAR MATASA DA BAYANAI
AHIP
KANO –NIJERIYA

TACEWA

MAIRO V. BELLO

DARAKTA /JAMI'AR KULA DA SHIRYE-SHIRYE NA AHIP.

**2000**

**MANUFOFI**

Bayan an Karanta Wannan littafi a qarshe za'a iya

1. Ba da aqalla ma'anoni biyar na shugabanci
2. Bayyana ire-iren shugabanci guda uku da misalai
3. Ba da abubuwa biyar da ake buqata ga shugaba
4. Yabawa gudunmawar shugaba
5. Tattaunawa filla-filla akan rashin amfanin girman kai ga shugaba.

**GABATARWA**

A koda yaushe rayuwa cikin tsari ta ke tafiya, daga sassauqar rayuwa har zuwa wadda ta zarta haka, a rayuwa akan tafiyar da abubuwa ne cikin tsari. Idan muka yi la'akari da rayuwar kiyashi duk da ya ke shine mafi qanqanta a cikin dabbobi za mu ga cewa shi ma ya na tafiyar da al'amuran shi ne cikin tsari, kamar dai yadda bil adama ya ke tafiyar da ta shi rayuwar. Saboda kowane al'amari na rayuwa a tsare ya ke. A sakamakon haka ne ma za mu ga cewa a duk lokacin da mutane su ka taru to lallai za a tarar suma suna da wasu dalilai na su, waxanda suka haxa da tunani iri guda da manufofi tare da samun buri iri xaya wanda a sakamakon haka ne ma wasu tambayoyi kan taso. Wasu daga cikin irin waxannan tambayoyin sun haxa da:

1. Menene takamaiman abin da mu ke so mu yi?
2. Yaya mu ke so mu yi shi?
3. yaushe za mu fara?
4. Wane ne zai yi?
5. Wane ne zai jagoranta?
6. Kuma a qarshe wane ne zai kula da abubuwa?

Babu makawa dole sai tambaya ta qarshe ta taso, wadda ba ita ba ce ta fi muhimmanci, amma kuma dole ana buqatar ta kafin a aiwatar da kowane irin shiri da aka tsara ake son gabatarwa.

Muhimmanci da wajabtar shugabanci ya taso ne a sakamakon manufofin da suka sanya mutane suka taru su ke da nufin cimmawa, saboda haka ne ma ake buqatar wani mutum ya tsarawa sauran mutanen yadda za su tafiyar da al'amuran su domin a samu a cimma manufofin da ake son cimmawa. Idan dai ba a samu shugaba nagari ba to haqiqa zai yi wuya ko da kuwa akwai mabiya masu qoqari a samu a cimma waxannan manufofi yadda ya kamata.

Shugabanci wani muhimmin vangare ne na sha'anin mulki, iya jagoranci wani muhimmin abu ne wanda zai taimaka a samar da tsari mai kyau. Ya zama wajibi ga shugabanni su yi aiki tuquru domin a samu a kai ga samun manufofin da qungiyar jama'a ke so.

Babban maqasudin shugabanci shi ne samun mabiya, sannan goyon bayan mabiya ne kan taimaka a samu shugaba. Har ila yau mutane kan bi bayan waxanda su ke ganin za su taimaka musu su cimma burikan su da buqatun su. Idan muka duba za mu ga cewa shugabanci yana tafiya hannu da hannu ne da kyautatawa.

## SHUGABANCI:

Kalmar Shugabanci ta samo asali ne daga Kalmar 'Shugaba' wanda Shugaba shi ne wanda zai zama tamkar jagora ga sauran jama'a waxanda su ke mabiya bayan sa.

Saboda haka shugabanci na nufin damar iya jan ra'ayin jama'a domin su samu su cimma wani buri. Za a iya cewa shugabanci wata hanya ce da akan bi wajen cusawa jama'a ra'ayi da kyautata musu domin a samu a cimma wasu manufofin da jama'ar su ke son cimmawa. Shugabanci ya na da bambanci da tursasawa sannan kuma akan yi nuni ne ba wai a tsoratar ba, tare da xaukar nauyi ba wai a turawa mabiya nauyi su kaxai ba.
Za mu iya cewa yin aiki tuquru tare da qoqarin cimma wani buri a kuma tabbatar da xorewar wannan buri.

Shugaba ya kan yi aiki ne domin taimakawa al'uma domin ganin cewa an cimma manufofin da ake son cimmawa ta hanyar yin amfani da irin baiwar da al'umar ta ke da shi. Har ila yau ya qunshi qarin qwarin gwiwa da kuma nusar da mabiya ba wai a tsoratar da su ba. Shugaba shi ne wanda zai shiga a dama da shi, ba ya daga cikin shugabanci xorawa mabiya nauyi, sannan kuma daga baya shugaban ya nuna cewa shi ne mai qoqarin.

## MA'ANAR SHUGABANCI

Masana daban-daban sun bada ma'anoni na shugabanci, Sai dai kowanne bayani ya yi qoqarin bayyana hali daban daban da akan fuskanta a yayin shugabanci. Amma kuma dukkansu kowanne yana da muhimmanci sosai. Sun kuma tavo wasu fuskoki na shugabantar jama'a amma duka suna da muhimmanci wajen fahimtar ma'anar shugabanci. Ga wasu daga cikin waxannan ma'anoni:

1. "Shugabanci qwazo ne na iya jagorantar mutane domin su iya cimma wani buri, da kuma samun cikakken goyon baya da haxin kai,shugabanci shi ne samun damar kawo canji tare

da gyaran halayya. "Munson (1921).Wannan ya na nuna mana cewa ya kamata duk wani shugaba ya taimaka wajen ganin cewa ya haxa kan mabiyan shi ba tare da samun varaka ba. Kamar misali a ce a wata makaranta za a yi gasa ta ajin da yi fi kyau, ana so makaranta ta shirya wa wannan gasa. Anan dole ne shugaban aji ya tabbatar da cewa koyaushe ajin na cikin tsabta sannan kuma waxanda suka iya shara sosai su ne za su yi sharar. Har ila yau shugaban ajin ne zai tabbatar da cewa an qawata ajin da kayan ado, ta hanyar sa waxanda su ka iya zane-zane da kwalliya su yi abubuwan da za su qawata ajin.

2. "Shugabanci wata irin dangantaka ce ta mulki da wani rukunin jama'a su ka yi amanna da shi, da tunanin cewa wani daga cikinsu za a samu wani ya zama shi ne mai tsara abubuwa a tsakanin 'yan wannan qungiyar". Janda (1960). Idan muka yi la'akari da wannan za mu samu cewa, dukkanin 'yan wannan aji an xauke su ne a matsayin 'yan qungiyar xaya da ke da iko akan mulkin wannan qungiyar. Shugaban wannan aji shi ke lura da kuma mutunta sauran a matsayin waxanda za su iya bada shawara da kuma kawo wasu shawarwarin a game da yadda rukunin jama'ar za su iya cin gasar. Misali waxanda aka danqawa amanar shara na iya shaidawa sauran yan ajin su cire takalmansu kafin su shiga aji, wanda ke da nauyin qawata aji kuma, na iya roqon kowa da kowa da ke ajin ya kawo hotunan tsofaffin kalanda domin qawata ajin da su.

3. "Shugabanci wani abu ne da ke tattare da xan'adam wanda kan haxa qungiyar wasu mutane wuri guda domin cimma wani buri". K. Davis (1962) A nan zamu iya cewa shugaban aji ne mutumin da ke riqe da ragamar sauran 'yan ajin, kuma shi ne ya ke nuna musu yadda za su yi su ci wannan gasa da suke da burin kasancewa na farko.

4. "Shugabanci ya qunshi haxa qarfi wuri guda, ta yadda idan kowanne mutum ya ba da ta shi gudunmawar, za a iya tafiyar da qarfin jama'a wajen gwagwarmayar cimma manufa iri guda" Pigors (1935). Wannan na nufin idan mutane suka haxu wuri guda domin cimma manufa xaya, to zamu samu cewa manufofin kowane daga cikin su da hazaqarsa da qwarewarsa su ne za su haxu su taimaka wajen cimma wannan manufa.

5. " Muddin akwai wani mutum a cikin mutane wanda shawarwarinsa sukan kasance masu muhimmanci, to lallai wannan mutumi yana da xabi'un shugabanci. Haka zalika muddin aka sami mutumin da al'umma ta yarda da irin shawarwarinsa, to lallai wannan mutumin

ya cancanci zama shugaba." Newcomb Turner and Converse (1965). Wannan na nuna cewa idan dai har aji ba zai ci gaba ba sai da taimakon 'yan wannan aji, to lallai kowa ma shugaba ne idan aka zo na sa fagen.

6. "Cikakken shugaba shine wanda yake da hazaqa da ilimin tare da ikon da zai iya canza abubuwa. Irin wannan mutum ba wai gwarzo ne kaxai ba yana la'akari da abubuwa, sannan kuma zai iya fuskantar kowace irin matsala da ta taso". Tichy and Devanna (1986). Misalin wannan yana magana ne akan wani shugaban xalibai da ya so ya kawo canji ga sauran 'yan makaranta. Da farko ana so shugaban xaliban ya kasance mai qoqari ne sannan kuma ya cancanci wannan muqami kuma zai iya xaukar wannan nauyin da ke tattare da wannan muqami. Sannan kuma har ila yau, yana da wayo da kuma kula da ra'ayoyin sauran xalibai, haka zalika ana so shugaba ya kasance zai iya yin aiki a kowane hali na rintsi da ya samu kan sa a ciki, wanda ke buqatar haquri da kuma dabaru a yayin takalar wannan matsala idan ta cakuxe.

7. "Lallai ne mu kaucewa kallon shugabanci a matsayin nasarar da mutum xaya ya samu saboda yanayin aikinmu na haxa qarfi da qarfe ne wuri guda" Nelson Hamdela (1992). A cikin wannan ma'ana da Nelson ya bayar, yana nuna mana cewa lallai shugabanci ba aikin mutum xaya ba ne, ya haxa da duk waxanda ke da hannu a ciki domin a samu akai ga cimma buri da samun nasara. Hakan ne ya ke nunawa shugabannin aji da shugabannin xalibai maza da na mata, da duk sauran masu muqamai daban-daban a makaranta cewa idan har babu mabiya to lallai babu shugaba. Sannan kuma ya na nuna mana duk wani abin da aka gudanar a lokacin mulkin wani to lallai kowa da kowa na da hannu a ciki.

## IRE-IREN TSARIN SHUGABANCI

Za'a iya karkasa tsarin shugabanci zuwa kashi uku ta la'akari da yadda ake gudanar da shawarwari da kuma irin tsarin halayen shugaba.

1. **TSARIN MULKI IRIN NA SARKI KO NA KAMA KARYA: (AUTOCRATIC):** A Wannan irin tsari na shugabanci, shugaba na shaidawa na qasa da shi ne kurum irin abubuwan da yake tsammani daga gare su, da kuma bada haske a game da abubuwan da ya ke so ayi, ya kuma nuna yadda ya ke so ayi su. Wannan tsarin mulki yana samar da

mabiya da kuma tsare-tsaren abubuwan da za a yi a rubuce. Sannan kuma shugabancin ya na tafiya ne da ikon ba da sakamako da damar yin horo. Akasari shugabannin cikin wannan tsarin mulki na hawa qaragar mulki ne ta hanyar yin amfani da qarfin su ko kuma ta hanyar gado. Za mu iya ganin misalan irin wannan tsari na shugabanci a Najeriya, kamar tsarin mulki na Sarki da muke da shi a yankin arewa, da tsari na Oba a yankin kudu da kuma tsari na Obi a yamma. Duk da cewa har yanzu ana amfani da irin wannan tsari sai dai kuma qarfin su ya ragu sosai, akasari sun fi qarfi ne ta wajen abubuwan da su ka shafi al'amuran al'adun gargajiya. Misali; ranakun wasu shagalgula, da naxin sarauta da sanarwar xaukar azumin watan Ramadan. Har ila yau Najeriya ta fuskanci irin wannan tsarin mulki a yayin mulkin soja, wanda ya xauki shekaru da dama ana tsarawa yan qasa yadda za su yi.

Wani misalin kuma shi ne na sarauniyar Ingila, da kuma sarkin Saudiya. Yana da muhimmanci a san cewa tsarin mulki na gargajiya ba tsarin mulkin kama karya ba ne,sauran misalan su ne na Sultan na Burnai da Sultan na Sokoto.

2. **DIMOKRAXIYYA:** Wannan tsari ne da aka fi sani da mulki na jama'a. A wannan tsari shugaba na tsayawa takara tare da wasu a zave shi, inda jama'a mafi rinjaye ke zavar wanda suke so. Irin wannan shugaba na tuntuvar sauran mabiya bayan shi ya nemi ra'ayoyin su. Wasu lokuta kuma har quri'a akan yi kafin ya yanke shawara. Ana kiran tsarin dimokraxiyya a matsayin tsarin mulkin jama'a wanda ya ke na jama'a ne kuma domin jama'a. Anan 'yan qasa suna da damar da za su zavi shugaban su, su kuma faxi ra'ayoyin su, su nemi 'yancin su, sannan kuma a ba su haqqoqin su. Sannan akwai 'yancin zaven irin tsawon lokacin da shugaba zai yi akan qaragar mulki, wannan ya na nuna mana cewa bayan shekaru huxu, akan bawa wasu dama su tsaya takarar neman shugaban qasa. Sannan yana sa mutane su yi aiki tuquru saboda suna da iya lokacin da za su yi a kan mulki kuma su na so idan wannan lokaci ya qare a sake zaven su. Wannan shine irin tsarin mulkin da aka fi amincewa da shi a duniya baki xaya. Har ila yau, qasar Amurka na gudanar da tsarin mulkin dimokraxiyya mafi kyau a duniya. Najeriya a yanzu tana gudanar da wannan tsarin mulki.

2. **TSARIN XAN BA RUWANA (LAISSER FAIRE):** Irin wannan shugabanci a wasu lokuta akan kwatanta shi da wani karin magana da ake cewa "Shugaba mai 'yanci, ya kan yi amfani da kaxan daga cikin ikon da ya ke da shi ne". In har ya yin ke nan, yana ba wa

na qasa da shi yanci sosai a al'amuransu, kuma irin waxannan shugabanni sun dogara ne kacokan ga na qasansu domin tsara manufofin su da kuma yadda za'a cimma manufofin. Suna ganin matsayinsu a matsayin na taimakawa abubuwan da mabiyan su ke zartarwa ne a tsakanin su da al'umar da ke waje. Wannan tsarin ba a fiye amfani da shi ba.

## ABUBUWAN DA AKE BUQATA DAGA IRE-IREN SHUGABANCI

### HALAYEN CIKAKKEN SHUGABA

1. Ilimi: Dole ne shugaba na-gari ya zama yana da ilimin da zai gudanar da aikinsa, hakan zai sa mabiya bayan sa su girmama shi tare da amincewa da duk wani hukunci da zai yanke.

2. Gaskiya da tsare mutuncin kai: Dole ne shugaba ya zama mai tsananin gaskiya, ya kamata na qasa da shi su iya bada shaidar Shuganbansu a matsayin mai gaskiya, ba wai game da aiki kawai ba har ma akan irin halayen sa. Shugaba na gari shi ne wanda ba ya aikata abubuwan da suka bijirewa yardar da aka yi masa a wurin aiki da kuma a sunan sa.

3. Yarda da kai: Dole ne shugaba nagari ya zama mutumin da ya yarda da kansa wajen fuskantar kowace irin matsala da za ta iya tasowa, duk kuwa irin wahalar da ke tattare da ita da kuma faxuwar gaba. Lallai ne ya nuna waxannan halaye ta yadda jama'a za su gani a cikin ayyukan shi da kuma halayen shi.

4. Qarfin tunkarar aiki da kuma neman nasara akai: Dole ne shugaba ya yi imani da aikin da yake yi. Da wannan ne zai ji daxin muqamin shi ya kuma girmama shi sannan kuma ya samu qwarin gwiwar gudanar da manufofin da ya sa a gaba.

4. Bayyana aikace-aikacensa: Wannan na nufin ya kamata shugaban kirki ya iya bayani ko bada rahoton aikace-aikacensa. Yana da muhimmanci ga shugaba ya samar da isassun bayanai ga na qasa da shi a game da aikace-aikacen qungiyar da kuma wuraren da aka samu matsaloli da kuma nasarorin da aka samu.

5. Jajircewa: Dole ne shugaba na gari ya zamo mai jajircewa a kowane irin yanayi, kada ya karaya har sai ya kai ga samun nasara. Shugaba na gari shine wanda: BA YA GAZAWA SAI DAI YA YI TA DAGEWA YANA QARAWA.

7. Mai qirqira: Ba ya tsayawa jiran wai sai mabiyan sa sun yi abu, sai dai kawai ayi kwatance da shi, ta yadda da ya kawo sabon tsari sai mabiya su karva hannu bi-biyu. wannan shine zai kawo ci gaba da samun nasara.

8. Sanin makamar hulxa da jama'a: Dole ne shugaba ya kyautata alaqar sa da al'umar da su ke tare da shi da kuma na waje,sannan kuma ya zamo mai la'akari da ra'ayoyin mabiyan sa.

9. Ladabtarwa da kyautatawa: Dole ne shugaba na kirki ya zama zai iya ladabtar da masu laifi, ya kuma sakawa waxanda su ka yi aiki tuquru, ma'ana waxanda suka yi abin kirki.

10. Mutuntawa: Xaya daga cikin alamun shugaba na gari shi ne mutunta na qasa da shi, kuma idan ka mutunta wasu, kai ma za a mutunta ka. Idan shugaba ya gaza mutunta mabiyanshi, to lallai zai yi wahala a gare shi su mutunta shi. Akan ce dukkan wanda ka ga ana mutunta shi, to shi ma ya mutunta kan shi ne. A wasu lokuta mukan ba da umarni ne kawai mu manta da mutuntaka, bayan kowa na da irin na shi ra'ayin kuma shima ya na so a ce yana ba da umarni, duk kuwa da irin matsayin shi. Saboda har sai mun mutunta sauran jama'a irin yadda muke so a mutunta mu kafin mu ma a mutunta mun.

<u>**NAUYE-NAUYE DA AYYUKAN SHUGABA:**</u>

1. Q**ara qaimi/Tayar da tsimi:** Aikin shugaba ne ya tada tsimin aiki a tsakanin na qasa da shi. Dole ne ya amince da qwazo da fafitikar kowane mutum domin a samu ci gaba da samar da yanayin da ya dace na aiki gadan-gadan. Dole ne shugaba ya gano mabiya masu sadaukar da kai, tare da qara musu qwarin guiwa ta hanyar qara masu girma da 'yan kyaututtuka. Wannan na qarawa ma'aikata qaimin aiki.

2. **kyautatawa:** Dole ne shugaba ya zamo mai ba da kyakkyawar sakaiya ga na qasa domin a kai ga cimma manufa. Ma'aikatan da suka nuna qwazo kamar yadda ake so, to a kyautata musu, sannan kuma waxanda su ka yi aiki tukuru a biya su da wasu kuxaxe, ko a qara musu girma a kuma yabe su fiye da sauran da ba su tavuka wani abu ba.

3. **Qarawa mabiya qaimi:** Dole ne shugaba ya qarawa mabiya qaimi ta hanyar kula da nusar da su ga aiki. Ya kuma nunawa mabiya muhimmancin cimma nasara

4. **Fayyace abubuwan da ake sa rai da su:** Ya kamata shugaba ya taimakawa na qasa da shi wajen fayyace abubuwan da ake sa rai da su, ta hanyar nuna musu abubuwan da kan kawo ci gaba da kuma sakamakon da ake so daga ko wane daga cikin su.

5. **Qwarin guiwa:** Wannan shine ba da qwarin guiwa ga na qasa domin su yi aiki tukuru ta hanyar yin amfani da abubuwa daban-daban misali, kyaututtuka, qarin wasu ‘yan kuxaxe, da kuma yabawa nasara ta hanyar yabo.

6. **Horo:** Ana sa ran shugaba ya horar ta re da bunqasa na qasa da shi domin qara qwazo da qara qaimi. Wannan na taimakawa wajen cimma buri da manufofin da aka sanya a gaba.

## MATSALOLIN DA KAN TASO DAGA BANGAREN SHUGABA.

Wannan ya fi yawa a kamfanoni da dama ko kuma rukunoni na ma’aikata, amma saboda canje-canjen da aka samu a ma’aikatu ya sanya irin wannan abu ya kau. A cikin irin wannan tsari shugaba ne kaxai ya ke da dama da ikon gabatar da abubuwa na rarraba ayyuka bisa son ran shi ba tare da ya yi la’akari da sauran mabiya bayan sa ba. Wannan tsari na shugabaci na tattare da wasu matsaloli da dama waxanda su ka haxa da:

1. **Tavarbarewar dabi’un ma’aikata**: Ana dakushewa ma’aikata qaimin su na son yin aiki wanda hakan kan jawo rashin samun yadda ake so. Wannan kan faru ne ba wai lallai a ma’aikatu kawai ba har ma a gidaje, domin idan har ka nunawa na qasa da kai cewa kai ne babba, to lallai za ka daqushe musu dabi’unsu na girmamawa.

2. **Rashin jituwa a wajen aiki**: Irin wannan tsarin shugabanci na jawo rashin jituwa da matsaloli a wajen aiki, idan har mabiya suka qi amincewa da umarnin shugabansu to rigima kan taso.

3. **Varna:** Idan ma'aikata ba su gamsu da halayen shugaban su ba, suna iya yin varnar kayan aiki su kuma qi tavuka komai a wajen aiki, tare da yin zagon qasa.

**WANE NE SHUGABA**

- Shugabanni Mutane ne da suka san me ake buqata, me ya cancanta da kuma sanin yadda za su jawo hankalin jama'a da samar da kayan aiki domin cimma manufofin da ake son cimmawa.
- Shugabanni su ne waxanda kan jawo ra'ayin jama'a da tunaninsu da halayen su da kuma ra'ayoyin su.
- Shugabanni sune zakaru a cikin al'amura, Mutane ne waxanda suka tabo inda ba a tava tavowa ba (Shiga inda ba a tava shiga ba). Su kan jagoranci sabbabbi da kuma abubuwan da ba asan su ba . Sune kan zamo kan gaba a wajen yin kamfen xin samun canji a ma'aikata.
- Shugabanni ne kan gina qungiyoyin, da jama'a kan ci gaba da faxaxa abubuwansu domin fahimtar matsaloli da alqibla, da kyautata xabi'ar su, wato, su zama masu koyo.

- **MANAJOJI NE KE YIN ABUBUWA DAIDAI, YA YIN DA SHUGABANNI KE YIN ABUBUWAN DA SUKA KAMATA;**

- **SHUGABA DILLALI NE MAI FATAN CIMMA NASARA**

Shugabanci da kuma kulawa abubuwa daban-daban ne waxanda ke buqatar zuciyoyi guda biyu da kuma basira daban-daban. Saboda masu kulawa suna da araha domin ya qunshi aikace-aikace ne, burin su kawai su san abin da za a yi da kuma yadda za a yi shi.A wani vangaren kuma, shugaba shi ne mai ba da umarni ga aikata abu, sannan kuma da yadda ma'aikata za ta kasance da abubuwan da za ta yi a gaba. Saboda haka aikin masu kulawa ne su kasance a wurin aiki su sa ido tare da yin la'akari da yadda ake gudanar da aikin. Shi ma shugaba ya na da ruwa da waxannan abubuwa, sai dai kuma ya fi mayar da hankali akan yadda za a bunqasa abubuwa ta hanyar sa ido akan abubuwan da ke faruwa ta hangen nesa da kuma ci gaban ma'aikata.

**MANAZARTA:**

1. Seventh Edition, management KooNT By: ODONNEL WEIHRICH.

2 Leaders who makes a Differience By: STEPHEN M. DOBBS.